# SHARUDDA GUDA HUDU NA SRI

# JAGORAR MANOMA NA SRI

## INGANTACCEN TSARIN NOMAN SHINKAFA NA (SRI)

…..Samar da kyakkyawan yanayi wa noman shinkafa

**"Bunkasa yanayi mai juriya wa noman shinkafa na Afirka ta Yamma"**

***(A ƙasashen Benin, Burkina Faso, Cote d'lvoire, Gambia, Ghana, Guinea Conakry, Liberia, Mali, Niger, Nigeria, Senegal, Sierra Leone da kuma Togo).***



**1. Samar Da Lafiyayyiyar Irin Shuka Mai Inganci A Farkon Lokaci**

- A tsoma irin shinkafar a cikin ruwa domin fitar da marasa inganci.
  - Tantancewa da tsoma iri a cikin ruwa kan hanzarta ingantuwar tsirowarsa.
- Kintsa inda za a yi rainon iri.
  - Inganta inda za a yi rainon irin kan sabbaba shukar ta yi ƙarko.
- A yi dashen irin tun tana da kwana 8 zuwa 13 da yafawa.
  - Hanzarta yin dashe da wurwuri kan ƙarfafa saurin yaɗo na yabanya.



Fig 1. Tantance iri ta tsomawa a ruwa domin ware maras inganci



Fig 2. Ingantaccen muhallin yafen iri na da mihimmanci a tsarin noma SRI



Fig. 3. Lafiyayyun kananan irinshinkafa domin dashe mai inganci

**2. A Taƙaita Gogayya Da Gasa A Tsakanin Shukoki**

- A shuka iri guda 1 a tazarar santimita 25 x 25 a jadawali na gida-gida
  - Hakan kan ƙarfafa girman shuka da saka jijiyoyi su kama ƙasa sosai.
  - Bayar da wadatacciyar tazara kan inganta shukar har ta yi yaɗo sosai.
  - Yin dashe a layi-layi kan samar da sauƙin yin noma a kan lokaci



Fig. 4. Dasa iri guda daya a kowane gurbin shuka.



Fig, 5. Yin shuka a tazarar santimita 25 x 25 na da muhimmanci



Fig. 6. Shuka a layi kan sauwaƙe noma ko ciron ciyawa

### 3. Samar Da Ingantacciyar Kasar Noma Mai Cike Da Takin Gargajiya.

- SRI takan ƙarfafa yin amfani da Takin Gargajiya.
- Hanyoyin samar da takin gargajiya sun haɗa da kashin shanu, awaki, tumaki, kaji da rubabbun ganyayyaki.
  - ➢ A barbaza takin gargajiya a yayin gudanar da sharar gona don a inganta ƙasar ta yadda za a sami ƙarin amfani.



Fig 7. An sarrafa ganye zuwa kasa



Fig. 8. Takin gargajiya domin barbawa a gona



Fig. 9. Kashin dabbobi domin barbazawa a gona na inganta yabanya

### 4. Alkinta (Tattalin) Ruwa A Tsanake – Tattalin Kasa Mai Laima

- A Kintsa Muhallin Da Kyau, A Daidaita Wurin Noma Tare Da Gina Madatsar Ruwa.
  - ➢ Daidaita muhallin noma kan ƙarfafi shuka ta girma da kuma jijiyoyinta za su kama ƙasa sosai.
  - ➢ Samar da madatsa kan inganta yadda ƙasar za ta iya riƙe ruwa tare da sabbaba samar da magudanan ruwa.
- Gwajin Fasalin Alkinta Jiƙakken Muhalli Noma Da Kuma Busasshe.
  - ➢ Dabarar jiƙawa da kuma busar da muhallinn kan inganta girman shukar da kuma bunƙasar tsaba.



Fig,10.Jika gonar bayan an yi dashe



Fig 11. Sai a bar gonar ta bushe



Fig 12.A sake yi wa gonar ban-ruwa .



Fig 13. A sake barin gonar ta bushe

### 5. Fi'idojin Tsarin Noma na SRI

- ➢ Samar da manyan jijiyoyi wa shuka domin domin ta ji daɗin zuƙo sinadarai.
- ➢ Samar da manyan rassa masu yawa domin haifar da tsaba masu yawa.
- ➢ Samar da ƙarin tushe masu cike da 'ya'ya domin samun yawan dammai .
- ➢ Yawan amfanin gona a lokacin girbi kan habaka kuɗin shiga wa manoma.



Fig 14. Manyan jijiyoyi na SRI



Fig 15. Manyan tushen shuka na SRI



Fig 16. Yawan rassan tsaba na SRI



Fig 17. Tsaba tsagwagwa a gonar SRI

---

Domin Neman Ƙarin Bayani, A Tuntubi:
The National Coordinator – RICOWAS Project - Nigeria
Email:umarumarabdullahi31@gmail.com.
u.umar@arcn.gov.ng.
Phone: 08036436114